Competitive Scramble is an Evil Ingenuity: Proceedings from the International Conference on the Biography and Songs of Alhaji Abubakar Kassu Zurmi in Heroic Poetry
A Publication of the Department of Nigerian Languages, Sokoto State University, Sokoto



| ISBN 978-978-62480-5-9 (Print) | ISBN 978-978-62480-5-9 (Online)
DOI: https://doi.org/10.65760/kassu.i1.35 Website: www.ssu.edu.ng |Issue 1 | April 2025|

# Salon Hira a Cikin Waƙar Nomau Namagarya da Waƙar Shayi Ɗan Gidan Labbo ta Kassu Zurmi

**Dano Balarabe Bunza,**
**Sani Yahaya Mafara**

Tsangayar Fasaha, Sashen Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami'ar Usmanu Ɗanfodiyo Sakkwato.
Abdu Gusau Polytechnic, Talata Mafara, Zamfara State

**Corresponding Author: Dano Balarabe Bunza** danobunza@gmail.com
Lambar Waya: 07035141980

**Tsakure**

*An rubuta maƙalar domin a fito da salon hira da ke cikin waƙoƙin da aka ambata a sama domin tabbatar da akwai shi a cikin waƙoƙin da ake magana a kai. Salon hira na nufin tattaunawa tsakanin makaɗi da masu sauraro ko da tauraro ko kuma da wasu a cikin waƙa dangane da wata matsala ko wani sha'ani da waƙa ta ƙunsa. Maƙalar ta nazarci salon hira da ke cikin waƙoƙin biyu, an kuma sami wasu nau'o'in salon hira da makaɗin ya yi amfani da su a cikin waƙoƙin nasa kamar yadda ƙumshiyar takardar ta bayyana. An yi haka ta fuskar farauto waƙoƙin da sauraren su da yin nazarin su, aka saurare su da kuma tsamo salon hira a cikinsu. Maƙalar ta gano cewa, akwai nau'o'in salon hira daban-daban a cikin waƙoƙin Kassu Zurmi, kuma an kawo su ɗaya bayan ɗaya tare da bayani da ingantatun misalai. An kawo misali na kowane nau'in salo da aka samu daga waƙoƙin da aka nazarta. Haka kuma, maƙalar ta gano cewa makaɗa Kassu haziƙi ne a fagen waƙa, kuma shi kaɗai ke rera waƙoƙinsa ba tare da taimakon 'yan amshi ba. Daga cikin nazarin da aka yi, maƙalar ta gano cewa salon hira muhimmi ne a cikin waƙoƙin baka domin yana ƙayatarwa sosai tare da jan hankulan masu sauraro dangane da abubuwan da suke gudana tsakanin jama'a a cikin waƙa.Kadadar wannan maƙala ita ce waƙoƙin biyu da aka zaɓa, wato, waƙar Nomau Namagarya da waƙar Shayi ɗan Gidan Labbo.*

**Copyright:** *Provided that the author(s) and the source are credited, noncommercial use of the article is allowed, including printing and distribution.*

## 1.1 Gabatarwa

Akan tsinci salon hira da dama a cikin waƙoƙin makaɗa daban-daban da suke rerawa a kan abubuwa mabambanta. An nazarci waƙar Nomau Namagarya da ta Shayi ɗan Gidan Labbo, kuma an tsinci salon hira a ciki kamar yadda aka bayyana a cikin wannan takarda. Salo ne mai jan hankalin mai sauraro tare da ƙayatar da shi dangane da abubuwan da ke faruwa tsakanin makaɗi da masu sauraro ko tsakanin makaɗi da tauraron da yake yi wa waƙa, ko kuma tsakanin makaɗi da wasu jama'a na daban dangane da wani lamari da ya faru, ko ke faruwa a tsakaninsu. An nazarci waƙoƙin biyu (Waƙar Nomau Namagarya da ta Shayi ɗan Gidan Labbo), sannan aka fito da hirar da aka samu a cikinsu a matsayin misali domin tabbatar da abin da aka faɗa a cikin matashiyar takardar. An fara da tattauna waƙar Nomau Namagarya, sannan aka biyo da waƙar Shayi ɗan GidanLabbo ta hanyar fito da hirarrakin da aka samu a cikinsu da kuma dalilan gudanar da su. Hira a cikin waƙa na nufin tattaunawa tsakanin wasu mutane a kan wata matsala ko wani al'amari da ya faru ko yake faruwa tsakanin makaɗi da wasu mutane. Haka kuma, hira na ɗaukar labartawa tsakanin makaɗi da wasu mutane kan wani al'amari da ya faru ko da yake faruwa a tsakaninsu. Domin jin irin hirarrakin da aka samu a cikin waƙoƙin biyu, ga yadda aka tsara takardar:

## 1.2 Ma'anar Hira

Ita ma kalmar hira an sami masana da suka bayar da ma'anarta gwargwadon fahimta. Daga cikinsu akwai Abdullahi Bayero Yahya da ya ce: "Idan baitocin waƙa suka ƙunshi muryar mai magana fiye daɗaya, wato mawaƙi ya ƙaddarta da shi da wani ne ke magana, ko kuwa wasu masu magana biyu ko fiye ne ke wa juna magana, to a fagen nazarin waƙa sai mu ce mawaƙi ya yi amfani da salon hira a cikin waƙarsa.Mai karatu ko sauraren waƙa zai ji muryoyi na masu magana a cikin waƙar.

Salon hira yakan taimaka wa mawaƙia ƙoƙarinsa na isar da saƙonsa ta hanyar sa mai saurare ko karatu ya zamo ya ƙara kusantar mawaƙin. Wato, sai mai saurare ya ji daga bakin waɗanda mawaƙi ke magana a kansu,ba wai daga bakin mawaƙin ba.

## 1.3 Taƙaitaccen Tarihin Makaɗa Abubakar Kassu Zurmi.

An haifi marigayi Abubakar Kassu Zurmi a garin a garin Kadawa ta ƙasar Zurmi da ke cikin ƙaramar Hukumar Mulkin Zurmi ta jihar Zamfara. Sunan mahaifinsa Mamman Ganga. Mahaifiyarsa kuwa, sunanta Maimuna. Kassu ya aurimat huɗu lokacin da yana raye. Sunan matarsa ta farko Ba'u.Matarsa ta biyu kuwa, ana kiran ta Gwamma. Sunan matarsa ta uku Inno. Matarsa ta huɗu ana kiran ta 'Yarɗiya. An yi waKassu laƙabi da ranar da aka haife shi ta lahadi wadda ta yi daidai da ranar kasuwar garin Dauran da ke cikin masarautar Zurmi. Kassu bai dogara ga kiɗa kaɗai ba domin yana noma da kiwo domin gudanar da lalurorin iyalansa. Yana kiɗa domin ya ilmantar, ya faɗakar da kuma wayar da kan al'umma. Kassu bai ɗauki kiɗi hanyar tara dukiya ba, domin waɗanda yake yi wa kiɗan ba su damu da tara dukiya ba, samun bajinta kaɗai ya dame su. Kafin rasuwar Kassu, ya kai shekara talatin ba yi kiɗa da waƙa ba. Ya yi wata rashin lafiya da ya kwanta a asibiti, sai dai daga baya ya sami sauƙi. Makaɗa Abubakar Kassu Zurmi ya rasu a shekarar 1983, yana da shekara saba'in da uku a duniya, mutuwa kuwa ita ce ƙarshen kowane al'amarin mutum.

## 1.5 Salon Hira a Cikin Waƙar Nomau Namagarya

An fara da wannan waƙar domin ita ce aka fara ambato kafin ta biyu, wato waƙar Shayi ɗan gidan Labbo. Dukkan waƙoƙin na ɗauke da salon hira a cikinsu kamar yadda bayani

zai tabbatar nan gaba kaɗan. An tsara hirarrakin da suka gudana tsakanin waɗanda mawaƙin ya fito da su da abubuwan da suka faɗa a cikin waƙarsa kamar haka:

### 1.5.1 Hira Tsakanin Kassu da Uban Balindo

Uban Balindo ya tarar da makaɗa Kassu a garin Kadawa inda ya gaya masa ana neman a ba shi doki, amma yana yi wa mutane jan rai. A nan Kassu ya ce, wa ka ba shi doki cikin garin Magara, in ba Nomau ba? A nan ma Kassu ya katse hanzarin samun doki daga Nomau saboda faɗar da ya yi cewa, Nomau ba ya da ko abin yin tuwo bale ya ba shi kyautar doki. Ga abin da ya ce:

Na dai yi tambaya cikin 'yan tauri,
Kuma na tambaya ga manyan makaɗa,
Wa an ka ba doki da gangami ba ni ba?
Wane ɗan tauri yay yi gangami da doki garinsu?
Doki da gangami sai Nomau Namagarya,
Don Uban Balindo shi ya' ishe ni hak Kadawa,
Yac ce "Kassu ana biɗak ka da doki ga ka kana alhwarma?
Nac ce ɗan karma ba ni ƙamnaƙ ƙarya,
Wa ka saye mani doki Magarya?
Nomau na ko abin tuwo ba ya da shi.

Da Kassu ya ji maganar Uban Balindo dangane da saye masa doki da kuma shakkunsa na samun doki daga wani da ba Nomau ba, sai da ya ce ba ya son ƙarya. A cikin tataunawar Kassu da Uban Balindo ga abin da ya gudana tsakaninsu kamar haka:

Sai yac ce "Ai da tarbace za a saye,
Da tarbace za a saye su wa su wa sunka shiga?
Na san dottiɓan Magarya zana mani su,
Cikinsu na san kowa, Na san mai iya yi,
Yac ce "Masalin Saraki ya ce a saye,
Ɗanmani Magaji ya ce a saye,
Gardaye Sanda ya ce a saye,
Sarkin hwawa Abdu ya ce a saye,
Kuma Labbo Sarkin Maƙera ya ce a saye.

Bayan Kassu ya yi saunar wani ya saye masa doki da ba Nomau ba, ya sa Uban Balindo ya gaya masa cewa, ta hanyar tarbace (haɗa kuɗi) za a saya masa wannan doki. Kassu dai bai gamsu ba sosai sai da ya tambayi abokin hirarsa cewa, ya san jama'ar Magarya musamman waɗanda suke dottiɓai ne. A kan haka, sai Kassu ya ce idan maganar da aka gaya masa gaskiya ce, a faɗa masa sunayen waɗanda za su yi tarbacen. A nan sai Uban Balindo ya zana masa dottiɓan Magarya mutum biyar waɗanda Kassu ya san da kowannensu na da ƙarfin sayen dokin shi kaɗai ba sai an haɗa ƙarfi ba. Jin haka ya sanya makaɗa Kassu kwasan nasa da nasa sai Magarya domin samun tabbacin dokin da aka ce za a ba shi.

### 1.5.2 Hira Tsakanin Kassu da Masu Sauraro

An sami hira tsakanin makaɗa Kassu da sauran mutane masu sauraron sa. Ya faɗa wa taron jama'a cewa, ya aminta da maganar dokin da aka yi masa. Daga nan sai ya kwashi turayensa ya nufi garin Magarya. Ga abin da ya faɗa dangane da wannan:

Ya zane man su dum mutum gudansu na iya dokin,

Sai nij ja turaye sai Magarya,
Ashe ba wanda yaj ji yag gani ƙarya ne,
Don a sha kiɗina banza,
Sai ana yi man na tumaki ana kashi na da ido,
'Yan yara suna yi man batun ban haushi.

Da Kassu ya isa Magarya sai ya tabbatar da gaskiyar maganar ko rashin kasancewar ta gaskiya. Ya gano zancen tarbace a saye masa doki ba gaskiya ba ce, an dai ruɗe shi ne, shi kuma ya nuna halinsu na makaɗa, wato kwaɗayi. An yi ne kawai domin a sha kiɗinsa ahaha. A nan Kassu ya ya gano har dubin wulaƙanci ake yi masa, kuma 'yan yara ƙanana na jifar sa da maganganun ban haushi. Daga nan sai Kassu ya juya hirarsa zuwa ga masu sauraro ko kuma taro kamar haka:

Bai dai samu dahi ba,
Sai ga Nomau ana ta gyaran kulki,
Da kambuna za a hwashe.

Zuwan Kassu garin Magarya bisa ga ruɗin da aka yi masa da maganar doki da gano maganar ƙarya ce. Ganin ba a yiwa Nomau Namagarya kara ba, sai ya shiga shirin in aikin da ba a san ɗan tauri da shi ba, wato fashi da makami duk da an san sun mallaki magani gwargwado. Ana cikin haka sai Kassu ya ci gaba da gaya wa masu saurare adda lamarin ya kaya kamar haka:

Da Allah yat tashi taimakon mu da doki,
Sahiya ta waye,
Tunda sahe yas sa buda ba ka ganin tahin hannunka,
Iska ko yaƙ zurƙaƙo ba ka jin ta ƙauye Magarya,
Sai nij ji gangami rariya-rariya,
Kun jiya Kadirawa jama'am Magarya,
Abin da Saraki yac ce a hwaɗa maku,
Kowa ya dibi gidanai in an ga sanwa wuri a kashe,
Ta ɗaka kau a sa makarai da yawa,
Allah ya raba mu da iskan ga lahiya,
Eh, sannan na Magaji yah hito za ya tciya,
'Yan yara sun yo shicci ƙanana-ƙanana,
Masu kama da na ƙumshe mahaihwa.

Kassu na ba masu sauraro labarin abin da ya faru da wayewar gari, cewa da Allah at tashi taimakon su da dokin da aka hana musu, tun da safe sai Allah a sa aka wayi gari da budar/hazon/ƙurar dako tafin hannu ba ta barin mutum a gani, kuma ga iska a fito mai tsananin ƙarfi, yana ƙara tamkar hadarin farkon damina ya taso. Da ganin haka sai Kassu ya ci gaba da ba masu saurarom sa labarin abin da a faru daga nan.
Ya faɗi cewa, maigari ya sa a yi shela cewa kowa ya duba cikin gidansa idan an aza sanwa waje a kashewuta, sanwar da ke cikin ɗaki kuma, a sa makarai da yawa kar iska ya kai wutar ga hakin ɗaki. Kowa na addu'a cewa, Allah ya raba mu da iskan ga lafiya. Ana cikin haka in ji Kassu sai tauraronsa ya fito zuwa batun ƙone garin Magarya. A lokacin Nomau ya yi daidai da 'yan yara sun yanko haki daga daji, ƙanana-ƙananan ƙulli. Har yanzu dai Kassu na nan na zuba wa masu sauraro hira in da ya ci gaba da faɗa musu abin da tauraronsa ya ci gaba da aikatawa kamar haka:

Yaɗ ɗoko dunƙule biyu kwatankwacin mushe,

Yal laƙe guda ga hamunta, yad dunguno guda ga murhu,
Ana ko kahhwa-kahhwa da wuta, sai nij ji mata na kuka,
Don Allah Saraki zaburo za ya hita x2,
Yara ashe sarki ba ya taƙama,
Ya ga abin da za ya hwaɗa ma gari,
Dole, yaka sai nig ga saraki an hito ba rawani,
....lahani ku kame mani shi x4,
'Yan saha sunka kame mashi shi.

Kassu ya ci gaba da ba da hirar da cewa, Namagarya ya ɗauko dunƙule biyu daga cikin hakin da 'yan yara suka yanko daji, yal laƙe ɗaya a hamutansa, ɗayan kuma sai ya je ga murhu mai wuta yal liƙa domin buƙatarsa. Ana cikin hannu ga gaba kar a ji tashin gobara sai kawai aka ji mata sun fashe da kuka suna kiran saraki da cewa ya fito mai faruwa ta faru. Nan Kassu ya gaya wa yaran cewa ashe sarki ba ya tsayi yin taƙama idan ya ga tashin hankali a cikin garinsa. Fitar da ta kama a kan tilas ba batun sanya rawani ake yi ba. Saraki na fitowa ya nemi a kame masa Namagarya. Ya faɗi ku kame mani shi har sau huɗu. Waɗanda saraki ya ba umurnin kame Nomau suka kama shi nan take. Daga nan sai hira ta koma tsakanin Nomau da saraki bayan an kama masa shi kamar haka:

### 1.5.3 Hira Tsakanin Saraki da Nomau Namagarya

Da aka kamewa Saraki Nomau, Saraki na isowa ga abin da suka tattauna tsakaninsu:

Dakanta ka jiya Nomau,
Yac ce "Ba in jiya ba jab bura' uba,
Ba ni ƙamnak kowa Magarya,
Duk ku rabi da ni.

Haƙiƙa Saraki ya zanta da Nomau bayan an kame masa shi, duk da yake ba doguwar zantawa ba ce. Tare da haka ana fahimtar cewa, zuciyar Nomau a sama take, kuma ba ya jin maganar kowa a wannan lokaci. Saraki ya ce wa Nomau ya dakata ya jiya. Nomau kuwa ya riga ya haure ba ya jin maganar kowa, nan take ya ce wa Saraki ba "Ba in jiya ba jab bura' uba" Magana ta ɓaci tunda Sarki na magana, Nomau ya yi masa baƙar magana ko kuma ya yi zagi. Zagin dai ba a cewa da Sarki Nomau yake kuma ba a cewa da wani ko wasu yake. Abin da ake iya fahimta dai zuciyar Nomau ta gurɓata, ba ya iya faɗin magana mai kyau a lokacin sai dai akasinta.

### 1.5.4 Hira Tsakanin Uban Balindo da Saraki

Uban Balindo shi ya yi sanadin zuwan Kassu garin Magarya domin jin an kwaɗaita masa doki. Da ya zo Magarya ya tarar da maganar doki ba gaskiya ba ce, sai ya birkita kwanci shi da tauraronsa, suka sake dabarar da ko babu doki a Magarya ,a tilas sai an ba shi. Da tauraronsa (Nomau) ya fara amfani da dabarar da makaɗa Kassu ya faɗa masa, a tilas saraki ya fito ba rawani. Kafin a kawo nan , Uban Balindo ya tafi wajen Saraki ya sheda masa abin da ya kawo Kassu Magarya cewa, doki ya kawo shi. Ga yadda hirarsa da Saraki ta kasance:

Wai kun ji Kassu doki yaka so,
Dokin wa?
Dokin Nomau,
Ah, to ya ba shi,

A'a Saraki ba haka tai ba,
Ai ku nac ce da tarbace za ku saye,
Yac ce la-la-la babu ruwana,
In don ni ko anini nau ba ya shiga,
Tunda Nomau ba ya raga ma kowa Magarya,
Sannan wani ba ya sa shi aiki ya tafi.

Uban Balindo ya gaya wa Saraki cewa, wai doki Kassu ke son a ba shi. Saraki ya tambaye shi dokin wa Kassu ka so? Ya fada masa dokin Nomau. Nan ya yi baƙar magana cewa ah, to ya ba shi dokin mana. Uban Balindo ya faɗa wa Saraki cewa ba haka maganar take ba. Ya gaya wa Kassu cewa Saraki da jama'arsa za su saye masa dokin. Nan take Saraki ya ce babu ruwansa da wannan magana, ko anininsa ba ya iya sakawa cikin saya wa Kassu doki, saboda ba ya raga wa kowa a garin Magarya. Ke nan,Nomau na iya ci wa kowa mutunci a garin daga Sarki har zuwa na ƙasa. Ma'ana, Nomau ba ya da ragowa, kuma babu mai sa shi wani aiki ya yi masa.

**1.5.5 Hira Tsakanin Kassu da Nomau**

A nan ne Kassu ya haɗe da Nomau yana zuga shi tare da faɗar Allah wadaran da shi da ƙarfinsa tunda bai tsinana komai ba cikin garin Magarya da komi kuma ga kowa. Haka kuma ba ya dakowa garin Magarya kuma, ba ya da kowa. A gaba kuma, sai suka ci gaba da hirarsu kamar haka:

He Allah ka wadden ƙarhin Nomau,
Mi ƙarhinka yad daɗa Namagarya?
Tunda ba ka da komi garin ga ba ka da kowa?
Ka ga dokin na baz zuwa gidaba ka yi shi ba,
Baba in sata kakai yi sata ka saye,
In kau ka ga ba ka sata yi hwashe,
Amma na baz zuwa gida ba ni da shi,
Baba kunya nika ji,
.................................................................,
Zakin na baz zuwa gida ba ka yi shi ba.

Kassu ya sheda wa Nomau cewa ba zai koma gida ba fa sai da dokin da ya kawo shi garin Magarya. Saboda haka, idan sata zai yi ko fashi dabara ta rage tasa, amma dai ba zai je gida ba sai tare da doki domin ya ce kunya yake ji a ji an kira shi a ba shi doki, sannan a ga ya komo ba da dokin ba. A kan haka ko shekaram maiki Kassu zai yi a garin Magarya sai dai ya yi ,matuƙar ba a ba shi dokin ba.

Nac ce in don sabadda ni ba ka hwashe,
Bari in ba ka shawara, in kab bi ta gobe dokin aka yi,
Magarya ko ba a da shi.
Allah dai ya kai mu gobe da sahe,
Karhe bakwai na sahiya,
Sai iskan nan ya taso,
Wanga na shiƙag gujiya,
Hina kwasan sansami,
Yana gamawa ya baƙi da babbaƙu kar-kar-kar,
Sai ka ji dottiɓai na gungu-gungu,
Suna Allah shi raba mu da iskan ga lahiya,
Wanga iska Allas sauwaƙa,

Sannan ebo wuta ga ragga ka hita,
Ba dai mai gini Magarya sai na rihewa,
To koma daz zuwa gidan Ɗan'aljanna,
Busa yab bura' uba, sai daji Namagarya,
Rantsuwa kat ta kasan.
Zama tare da 'yan gudummuwa za ni hita,
Wuta nah hissan, bila'i ko ta.

Hirar Kassu da Nomau ta ci gaba a inda Kassu ya gaya wa Nomau cewa, idan dai saboda shi zai yi fashi da makami, to zai yi ba, amma zai ba shi shawara, idan ya yi amfani da shawarar, tilas gobe ko babu doki Magarya sai an ba shi. Ya roƙi Allah ya kai rayuwarsu gobe da safe. Daga nan sai Kassu ya juya akalar hirarsa zuwa ga masu sauraro yana faɗa musu cewa, wayewar gari ke da wuya, da ƙarfe bakwai na safe, sai iska ya tasoirin shiƙag gujiya yana kwasan sansami iri daban-daban yana tafiya da su. A ci gaba da hirarsa da masu sauraro, yana gaya musu cewa, sai dottiɓan Magarya suka yi gungu-gungu suna addu'ar Allah ya raba su da iskan lafiya, suna fadar wannan iskan Allah ya sauwaƙa.
Kassu ya ba Nomau shawara cewa, da an shiga wannan hali, ya ɗebo wuta ga ragga kawai ya fita, ko banza ba mai gini Magarya sai na rihewa.Ya ba shi shawara ta biyu cewa ya koma daga gidan Ɗan'aljanna, ya hura 'yab bura'uba ta kama sai daji (ƙarshen gari). Ya yi hakan domin kar tsantsuwar da ya yi kan cewa ba ya komawa gida face da doki, ta kama shi wataƙila ya mutu. Ya faɗi cewa da wutar ta kama, babu shakka tare da 'an gudummuwa za shi fita ya bar garin, domin in ya koma ba da doki ba, aka ji gobara aka yi garin Magarya, maganar doki na zama ƙarama a kan ta ƙonewar gari ƙurmus. Daga wannan gaɓa kuma, sai hira ta harɗe tsakanin, Kassu da taurarunsa kamar haka:

Yac ce "Kassu shawararka ita za ni biya,
Baba in ka bita gobe dokin aka yi Magarya ko ba a da shi,
A'ah, hnm,
Ina hwaɗi in dai ba a son ka tungag ga hita,
Nomau in ba su son katungag ga hita,
Yac ce "Ina hita Mai kasuwa,
To amma hwa ba da alheri ba,
Bari ko an hani ni yanzu da rana,
Sai iskan sha biyun dare ya taso,
Sannan za ni kunna 'yab bura' uba,
Magarya sannan da ko ɗiyansu wasu ba su hita.

Nan take da jin shawar da makaɗa ya ba Noma, sai ya buɗa baki ya ce shawarar Kassu zai yi amfani da ita kuma ya aminta. Shi kuma Kassu ya ce, lalle idan ya bi wannan shawara, babu shakka za a sami dokin nan gobe, ko babu shi garin Magarya. Haka ya ci gaba da ba Nomau shawarar cewa, idan dai ba a son sa cikin tungar Magarya, to ya fita ya huta wa rayuwarsa. Nan take Nomau ya amince da shawarar barin gari sai ya ce, lalle zai fita garin Magarya amma fa ba fitan alheri ba. Wannan zuga ce Kassu ya yi wa Nomau domin ya ingiza shi zuwa ga aikata abin da ya ba shi shawrar aikatawa. Ya ce ya bari ko an hana shi aikata ɓarnar da ya yi niyyar aikatawa da rana, zai bari sai iskan ƙarfe goma sha biyun dare ya taso, lokacin zai kunna ta daidai an yi kwana a tashi ba don Allah ba. Ya faɗi zai yi haka ne domin har da wasu 'ya'yansu su mutu.

### 1.5.6 Hira Tsakanin Magaji da Saraki

An sami hira tsakanin Magaji da Saraki a kan maganar da ya yi ta cewa ba ya sa ko anininsa, kuma Nomau ya je ya kunna wutar ya yi duk abin da ya yi nufi. Jin wannan magana ta Saraki sai Magaji ya ce assha Saraki kamar haka:

Sai Magaji yac ce "Assha Saraki,
Dottijo da kai?
Ba ka tcinkaya' abin da an nesa sai ƙarƙashin ƙahwahunka?
To bari dai in hwaɗa ma gaskiya,
Nomau dai ya hi mu gaskiya,
Komi kag ga ya yi mu munka biɗa,
Yanzu dai ba ɗan doki ba na tauri,
Nan Magarya ko mota munka so saye ba mu saye?
To in ya kai mu yab baro,
Ban ga abin da za ka ɗiba ba garai,
Wandara sai dai a ƙoshi ɗamri a sakai.

Magaji ya ci gaba da jan hankalin Saraki da cewa, kasancewarsa dottijo ya yi kuskuren furta maganar da ya gaya wa Nomau Namagarya. Me ya sa ba ya duban abin da ke tafe, sai dai wanda ke kusa da shi? Ya gaya masa cewa, Nomau fa ya fi su gaskiya, kuma duk abin da ya yi mu muka ja wa kanmu.Ya ce ba ma dokin tauri ba, a garin Magarya ko mota suke son saye ba su saye bale doki? Idan ya bari Nomau ya aikata abin da ya yi niyya, babu shakka banza ta sha su , domin bai ga abin daSaraki zai ɗiba ba ga Nomau tunda hasali ma matsiyaci ne. Ko da za a yi,ba za zarce a ɗaure ba, kuma idan aka gaji da ɗaurin tilas a sake shi. Abubuwan da muka jitsakanin mabambantan mutanen da ajka kawo tattaunawa tsakaninsu ,ita ce hira. Makaɗa Kassu ya yi amfani da wasu dabaru na ƙulla wannan labari, shi ya sanya aka kira shi salon hira a cikin waƙar Nomau Namagarya

## 1.2 Salon Hira a Cikin Waƙar Shayi ɗan Gidan Laabbo

Waƙa ta biyu da aka fito da salon hira a cikinta ita ce, waƙar Shayi ɗan gidan Labbo. Akwai salon hira a cikin waƙar gwargwado a inda aka sami makaɗa Kassu na hira da wasu ko wani. Ga abin da aka samu na hira a cikin waƙar kamar haka:

### 1.2.1 Hira Tsakani Kassu da Masu Sauraro/Taro

Kamar yadda aka sami hira a cikin waƙar Nomau Namagarya tsakanin Kassu da masu sauraro, haka ma an same shi a cikin wannan waƙa ta Shayi ɗan gidan Labbo kamar haka:

Mai kwana ya tashi mai tahiya kau shi dakata shi kau,
Ku tashi kun ji kiɗin Shayi ɗan gidan Labbo,
Na Abu ɗan baƙin daji,
Ku hwalka na kai ga masu ɗan gashi,
Lalle Shayaya ad da ɗan gashi,
Ya yi biɗa' amre bara sai da yas samu,
Iro ya kai ta gidan maigidansu yah hwaɗi,
Am mutu yab bash shi ba abin amren kana ba hatcin ɗiba,
Sai an game da Labbo yana tattalin ɗiyan dangi,
To daɗa amren Shayaya Labbo ya wahala,
Ran amren Shayaya Labbo yai yawo, yai yawo,
Amren Shayaya Labbo ya yi jidali garin biɗab bashi,

Ya sha raɓa kamak karen daji,
Ya sha rana kama tudun ɗaki,
Labbo ya takwaikwaye walki shina ginah hanya,
Maidabo Ɗan'auta za ya ba shi yah hwasa,
Aha, kun yi gidan Bawa Ɗangaladima,
Sai da Bawa yab ba su sai Taɗari takw kwace.

Kassu ya fara jan hankalin masu sauraro da cewa, duk wanda ke kwance yana kwana ya tashi idan yana son jin labarin Shayi ɗan gidan Labbo. Wanda ke kan hanya yana tafiya shi ma idan yana son jin zaren labarin Shayi, sai ya tsaya cik ya karkaɗe kunnuwansa domin ya sha labari. Ya ƙara da cewa masu kwana su farka domin ya kai ga masu ɗan gashi. Masu ɗan gashi da yake nufi a nan shi ne Shayi. Idan kuma mutaneyake nufi da dama, yana nufin Shayi da jama'arsa (danginsa irin Labbo da sauransu). Ya fara ba da hirar Shayi ga masu sauraro cewa, Shayi ya yi neman mata shekarar da ta gabata kuma, sai da yas samu, amma da ya kai ta gidan maigidansu sai ya faɗi mai nufin an sami matsala.Matsalar da aka samu ita ce Kassu ya faɗa cewa, am mutu am bar shi babu abin yin auren kuma babu hatsin ci. Nasarar da aka yi ita ce, an yi dace Labbo na da halin kirki na kula da 'ya'an 'yan uwa. Lokacin auren Shayi Labbo ya wahala kuma ya yi yawo ƙwarai na ya je nan nema a hana shi, ya je can a hana shi. Hakakuma Kassu ya faɗa a cikin hirar da yake yi da masu sauraro cewa, Labbo ya sha wahalar neman bashi lokacin auren ɗansa Shayi. Ya bayyana wa masu sauraro cewa Labbo ya sha raɓa kamar karen daji, kuma ya sha rana kamar tudun ɗaki. Ba wannan kaɗai ba, masu sauraro sun cira daga bakin makaɗa Kassu cewa, har walki Labbo ke ɗaurawa idan yana ginan hanya. Ginan hanya a nan na nufin yawan tafiyar da yake yi na je nan, je can domin nema wa Shayi matar aure, kuma saboda rashin tagomashinsa, duk wurin da aka tunkara sai maganar ta watse. Kassu ya ba masu sauraro labarin cewa, akwai wani mutum mai suna Maidabo Ɗan'auta har zai ba su, kuma ya fasa. Daga nan, sai suka je gidan Bawa Ɗangaladima, har ya ba su sai wata mata mai suna Taɗari taƙw ƙwace. Ga cikon hirar daga makaɗin:

### 1.2.2 Hira Tsakanin Taɗari da Labbo

A cikin waƙar har yanzu dai an sami hira tsakanin Taɗari da Labbo maga'ishin Shayi, lokacin da ya je nema wa Shayi matar aure. Ga yadda hirar ta kasance tsakaninsu:

Tac ce sabilin Shayaya ba a bashe su,
Ɗannema bai raga ma kowa ba,
Wata 'yag gona garai cikin tabki,
Bara yat tashi yana kashin awakinmu,
Tac ce misalin ƙato gudum awash Shayi,
Ƙaton ka biɗab bashi?
Labbo yac ce ƙaton na banza ne,
Komi yab biɗa na mata ne,
Dum mata sun bi Iro sun koɗe.

Lokacin da Labbo ya je nema wa Shayi aure wajen Bawa, har an bayar sai Taɗari taƙ ƙwace saboda bai raga wa kowa. A nan ana nufin Shayi ba ya da rogowa. Ta ƙara sheda wa Labbo cewa, yana da wata 'ar gona cikin tabki, sai ya ci gaba da kashe musu awaki,maiyiwuwa saboda shiga gonarsa da suke yi. A cikin hirar Taɗari ta ƙara da cewa tare da tambaya, wai ƙato irin Shayi mai ƙarfi a ce sai an je biɗo masa bashi? Nan kuma Labbo ya mayar mata da bayanin cewa,Shayi ƙaton banza ne, sannan duk biɗarsa tana wajen mata, kuma

duk mata sun bi Shayi sun sun koɗe. Wannan na nuna Shayi na neman mata kuma ga dukkan alamu sun kaɗe masa jininsa.

Hirar ta ci gaba a inda Kassu ya ƙara ba da labarin cewa:

Kamas su buga ga su nan cikin gebe,
Nac ce musu kak ku buga ya ishe ku jiɗawwa,
Ai ko Shayaya munka sha daula,
Mun sha zabbi gaɗan gidan Labbo,
Nic ce ma 'yan yarana ku sha ahaha ce tunda ba ya maishe su,
Katakoro Iro na Ummaru mai guzurin kunya,
Ko da za mu watcikkewa kana uwayen matan ga sunka jawo ni
Ga ni ga matan ga ga uwayensu mu kaɗai cikin zaure.

A nan kuma, Kassu ne ke zantawada'yan matan da suka tarbo Shayi tun cikin gebe, suna musu da juna a kan kowace daga cikinsu tana son Shayi. Shi ne Kassu ke ba masu sauraro labarin cewa 'yan mata sun rinƙa rigima kamar su buga saboda kowace daga cikinsu ta yi tsaye ita ke son Shayi. Kassu ya ce musu su bi a hankali kar su bugi juna, kowace daga cikinsu na samun Shayi. Shi dai Kassu ya ci gaba da ba da labarin irin tarbon arziki da aka yi musu domin an yi musu goma sha biyu na arziki. Ya ba da labarin sun sha daula domin sun sha zabbi, har da faɗa wa yaransa su sha banza ta ta samu. A can baya ma ya faɗa a cikin hirarsu cewa, ya har da ɗan nalutsa da mai sosai a cikin liyafar da aka kawo musu.

**1.2.3 Tsakanin 'Yan Mata**

Ana sane da cewa, duk lokacin da mutum ya ga abin da yake so da ƙauna, jin ake kamar ya ƙwata. Wannan ya sanya rigima ta kusa faruwa tsakaninsu har sai da Kassu ya shiga tsakani. Hirar da ta gudana tsakanin 'yan mata masu son Nomau 'yar ƙil ce kamar haka:

I wan in Shayi ni ka jishshe shi,
A'a kina ƙarya na riga ki zaɓo shi,

Ɗaya daga cikin 'yan matan ganin Shayi ke da wuya sai ta ce ita za ta jidda/saukar da Shayi don tana son sa. Ita kuma ɗayar ta ce, kin faɗi ƙarya domin na riga ki zaɓar sa. A nan rigima ta kaule kamar su buga, sai da Kassu ya shiga tsakaninsu. Da ba don Kassu ba, ba a san abin da zai faru tsakaninsu ba. Wannan ce hirar da ta shiga tsakanin "yan matan da ke ra'ayin Nomau lokacin da suka hango shi tun daga cikin gebe/goru.

**1.2.4 Kassu da Iyayen 'Yan Mata**

Wannan ce hira ta ƙarshe da ta gudana a cikin waƙar Nomau Namagarya da Kassu ya yi wa Shayi ɗan gidan Labbo. An ji cewa a sama iyayen 'yan mata sun keɓanta da Kassu a cikin zaure domin su yi masa tambayoyi dangane da al'amarin Shayi dangane da baikonsu da suka warware da masu neman su na farko. Ashe ko Shayi na iya auren ɗaya daga cikin 'yan matan bale su da yawa? Ga yadda hirar ta gudana tsakanin Kassu da iyayen 'yan matan da ke son Nomau Namagarya.

Kassu amana' Allah ka ba mu labari,
Nic ce wane labari?
Labarin Shayi ɗan gidan Labbo,
'Yan mata sun walwale baikonsu sun ce Shayaya za shi rankonsu,
Shi muka son ka ba mu labari in akwai gidan kirki,
Nic ce yau ko dottiɓe kun damarshe ni,
Ya hi ku koma ku sake ɗan sheda,

Na Abu ɗan uwana ne,
Mutum ko bai sheda ɗan uwansa ko hwada.

Iyayen yara ‘yanmata da Kassu na zaune a zaure, sai suka fara kai Kassu ga Allah, cewa sun ba shi amana kuma sun sa shi gaba, ya faɗa musu gaskiya game da Shayi saboda ɗiyansu sun yi tsaye ba su auren kowa sai Shayi. Sun nemi Kassu ya ba su labari na tsakani da Allah, sai ya ce labarin me? Iyayen ‘yan mata suka ce labarin Shayi ɗan gidan Labbo, domin ‘yan mata sun walwale baikon da aka yi musu da wasu, yanzu Shayi suke so. A kan wannan ne suke buƙatar jin idan akwai gidan kirki. Kai tsaye Kassu ya ce yau kan sun damarshe shi, wato sun ritashi bai san yadda zai yi ba saboda wasu dalilai da ya ambata. Na farko dai ya ce ya fi kyau su sami wani da ba shi ba su tambaye shi. Na biyu kuma ya ce Shayi ɗan uwansa ne, kuma mutum ba ya shedar ɗan uwansa ko hwada. Daga nan sai hirar da Kassu ke yi da iyayen ‘yan mata ta ci gaba kamar haka:

Kassu amana’ Allah ka ba mu labari,
Ni kau amana’ Allan ga ɗai ka sha min kai,
In na bi amana’ Allan ga na yi ɓatanci,
Kuma in tuna ban cin amana’Allah saboda tantiri,
Amma hwa ku ba shi in kuna ba shi,
Na Abu Shayi dai ɗa ne,
Sunka ce “Ba haka munka so ba ɗan yaro,
Ai mun san ɗa ne tunda anka haihe shi,
Ba mu labari in akwai gidan kirki”,
Nac ce gaskiyakka dottijo,

Iyayen ‘yan mata suka liƙe waKassu kuma suka haɗa shi da Allah ya ba su labarin abin da ya sani game da Nomau domin su ba su sani ba. Kassu ya san Shayi domin tauraronsa ne, ya san halayensa sosai, shi ya sa ya nuna damuwa da aka haɗa shi da Allah ya faɗa musu gaskiya. Wannan ya sanya shi faɗar cewa, shi fa amana’ Allan ga ɗai ka sha mai kai. A taƙaice, bai ji daɗin da suka haɗa shi da Allah domin ya gaya musu gaskiya dangane da Nomau ba. Ya fadi cewa, idan ya fadi gaskiyar da aka neme shi da ya faɗa, babu shakka ɓarna za ta faru domin Shayi zai rasa ‘yan matan.Haka kuma ya ce ba zai ci amanar Allah ya ɓoye gaskiya saboda wani tantiri irin Shayi ba. Buɗa bakin Kassu ke da wuya,sai ya gaya musu cewa, su ba Shayi idan suna ba shi, domin dai ɗa ne kamar kowa. Da suka ji haka daga baki Kassu, sai suka ce masa ba haka munka so ba ɗan yaro, domin mun san ɗa ne tunda haihuwarsa aka yi. Abin da suke buƙata ya ba su labari idan gidan su Shayi gidan kirki ne. Nan sai ya ce wa dottijon lalle ya fadi gaskiya. Don haka sai Kassu ya yi ƙarfin hali ya fadi wani abu game da Shayi saboda kar ya yi ƙarya girmansa ya fadi ga dottiɓan nan. Hirarsu ta ci gab kamar haka:

Mutum ko ba za ya kai ɗiyatai ba gidan da ba abin kirki,
Amma hwa ku ba shi in kuna ba shi,
Ɗiyad dottiɓai kaɗai ka amren Shayaya ɗan gidan Labbo,
Ɗan gidan Labbo na Abu kowa’ amre shi ita ka cishe shi,
Ta biya kuɗɗin garin karen kyarso,
Sannan ta yi mai abin ruhwa ko rab....,
Kana ta koma ta yi dabbarin abin ɗamri,
Dottijo yat tashi yab buge riga yai cikin zaure

.

Kassu ya fahimci manufar dottiɓan dangane da tambayoyin da suke yi masa, har aka kai yana goyon bayansu a kan binciken da suke yi masa. Ya aminta da su cewa ba abu ne mai daɗi ba mutum ya kai ɗiyarsa gidan da ba na kirki ba. Wannan ya sa Kassu ya gaya musu cewa, idan suna da niyyar ba Shayi aure su ba shi. Ya faɗa musu cewa, ɗiyar mutumin kirki kaɗai ke iya auren Shayi, domin kowa'auri Shayi ita za ta ci gaba da ciyar da shi, ba shi zai ciyar da ita ba. Haka kuma, a cikin hirar da suke yi ya ƙara tabbatar musu cewa, sai ta biya wasu kuɗin karen zuwansa farauta. Ya ƙara musu da cewa, ita za ta saya masa zanen rufa domin su san cewa ba batun saya mata tufafi ba ne. Da dottijo ya ji haka, sai ya tashi ya buge/ kakkaɓe rigarsa ya bar Kassu nan ko sai an jima babu, saboda gamsuwar da ya yi da bayanin Kassu daga.na cimma abin da yake son ji.

## 1.3 Sakamakon Bincike

A nan aka kawo ƙarshen wannan bincike kuma an gano abubuwa da dama a ciki. Daga cikin abubuwan da maƙalar ta gano akwai rashin 'yan amshi ga makaɗa Kassu. Haka kuma an gano cewa, ba a cika samun ɓarayi a cikin 'yan tauri ba. An ga haka a inda Kassu ya faɗa wa Shayi cewa, ba zai koma gida ba matuƙar ba dokinaka ba shi ba. Daga cikin abubuwan da maƙalar ta gano kuma, akwai matuƙar lalaci ga wasu 'yan tauri irin Shayi da har da'yan uwansa ba su yaba da halinsa ba.Haka kuma an gano cewa harakar tauri kaɗai ta dame su na a yi suna a cikin harakar, sannan ba a damu da talauci ba domin an riga an saba. Tare da hak, an gano Kassu ya san miyagun ɗabi'u, kuma yana gudun taurarinsa da faɗawaa ciki.A ƙarshe, an gano cewa dangi na samun damuwa idan ɗan uwansu ya nakkasa kamar yadda Kassu ya bayyana lalacewar Nomau a bainar jama'a.

## 1.4 Kammalawa

An dubi salon hira a cikin waƙoƙi biyu da suka haɗa da waƙar Nomau Namagarya da waƙar Shayi ɗan Gidan Labbo. An fara da tattauna waƙar Nomau Namagarya da aka dubi abubuwa da suka haɗa da hira tsakanin Kassu da Uban Balindo da tsakanin Kassu da masu sauraro da hira tsakanin Saraki da Nomau Namagarya da hira tsakanin Uban Balindo da Saraki. Haka znacen hirar ya ci gaba in da aka kawo hirar da ta gudana tsakanin Kassu da Nomau Namagarya da kuma hirar da ta shiga tsakanin Magaji da Saraki a zaman hira ta ƙarshe da aka kawo daga cikin waƙar Nomau Namagarya.
A waƙa ta biyu, wato waƙar Shayi ɗan Gidan Labbo da aka sami hirarrakin da suka gudana tsakanin wasu da wani ko kuma wani da wani. An kawo hirar da ta gudana tsakanin Kassu da masu sauraro da kuma hirar da ta gudana tsakanin Taɗari da Labbo lokacin da ya je nema wa Shayi aure. Bayan an ba shi auren da ya biɗa wa Shayi, Taɗari ta amshe ta hana wannan aure. An kawo hirar da ta gudana tsakanin 'yan matan da suka tsaya kai da ƙafa suna son Shayi. A ƙarshe an kawo hirar da ta gudana tsakanin Kassu da iyayen 'yan mata dangane da tambayoyin da suka yi wa Kassu dangane da jin labarin gidan su Shayi. A nan maka tuƙe maƙalar kan bayanan da suka gabata.

© Department of Nigerian Languages, Sokoto State University, Sokoto 

**Manazarta**


Abba da Zulyadaini (2000). *Nazari Kan Waƙar Baka Ta Hausa.* Gaskiya Corporation LTD, Zaria.

Bunza, A.M. (2009). Narambaɗa. Ibrash Islamic Publications Centre Limited Lagos.

Bunza, A. M. (2015). *In Ba Ka San Gari Ba Saurari Daka: Nazarin Tafashen Sata a Cikin Kiin Ɓarayi na Muhammadu Gambo Fadaga.* TIWAL Printing Press Cairo.

CNHN, (2006), *Kamusun Hausa Kano. Jami'ar Bayero, Kano.*

Ɗangambo, A. (1989). *Rabe-raben Adabin Hausa da Muhimmancinsa ga Rayuwar Hausawa.* Kano Triumph.

Ɗangambo, A. (2007). *Ɗaurayar Gadon Feɗe Waƙa*. Amana Publishers Ltd Zaria, Kaduna, State.

Gusau, S. M. (2003). *Jagoran Nazari Waƙar Baka.* Kano, Benchmark Publishers Limited.

Gusau, S.M. (1993). *Jagoran Nazarin Waƙar Baka*. Benchmark Publishers. Limited-Kano.

Gusau, S.M. (2009). *Diwanin Waƙoƙin Baka. Zaɓaɓɓun Matanoni na Waƙoƙin Baka na Hausa.* Century Research and Publishing Limited Kano-Nigeria.

Magaji, A. (2016). *Kassu Zurmi da Waƙoƙinsa.* Spectrum Books Limited, Spectrum House, Ring Road, P.M.B.5612, Ibadan-Nigeria

Skinner, N. (1980), An Anthology Of Hausa Literature, N.N.P.C.

Yahya, A.B. (1997) Jigon Nazarin Waƙa. Fisbas Media Service, Kaduna.